# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kwallon ƙafa salon Afirka
## Kashi na ɗaya: 'Yan wasa uku, manufa ɗaya


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya tace: | Ludger Schadomsky da Maja Braun |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Zakari: | ɗan shekara 14 |
| Shehu: | ɗan shekara 14 |
| Anti Lily: | 'yar shekara 33 |
| Safina: | 'yar shekara 13 |
| John: | ɗan shekara 15 |
| Honourable Gambo: | ɗan shekara 55 |
| 'Yar jarida: | 'yar shekara 25 |
| Wani mutum: | ɗan shekara 30 |

**MAI GABATARWA:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin wani sabon shirinmu na "Ji Ka Karu". A wannan karon, za mu kawo muku jerin shirye-shirye ne har kala goma, wanda za ku ji labarin wasu yara su uku, Zakari, mabaraci, John, ɗan wani ɗan siyasa mai kuɗi, da Safina, wata yarinya da ta baro ƙauye ta koma birnin Gabas. Kowanne daga cikinsu na fatan ganin cewa ya zama ɗan wasan ƙwallon ƙafa da zai yi fice a duniya. Amma wace hanya za su bi don ganin cewa burinsu ya cika? Sai ku biyo mu sannu a hankali, ku saurari yadda wannan wasa da aka sa wa suna "Kwallon ƙafa salon Africa". Shiri na farko na da taken "'Yan wasa uku, manufa ɗaya". Za mu faro ne daga titunan birnin Gabas.

**Fitowa ta 1: A garin Gabas**

Shehu, Zakari

**ZAKARI da SHEHU:** *suna bara*

**ZAKARI:** Wash! Gaskiya na gaji Shehu. Tun safe muke baran nan, muna zaune wuri ɗaya, kowa ya kalle mu ya san yunwa muke ji, amma kamar ba wanda ya damu da halin da muke ciki. Sule biyu fa kacal! Abin da muka samu ke nan kuwa?

**SHEHU:** E, sule biyu kawai. Kuma fa Zaks, kar ka manta cewa kuskure matar ta yi suka faɗo saboda tana sauri. Bacin haka da har yanzu ba kome a cikin kwanon baranmu, kuma ka san abin da haka yake nufi. In ba kome…

**ZAKARI DA SHEHU:** …yunwa!

**ZAKARI:** Amma na so a ce mun bi ta da gudu mun mai da mata kuɗinta. Wa ya sani? Wataƙila da ta saka mana da…

**SHEHU:** "Na gode!" da abin da za ta ce ke nan fa kawai. "Na gode", sannan taf!taf!taf!, shi ke nan haka za ta yi tafiyarta. Ka farka daga barcin da kake yi, Zaks! Gantali muke yi a kan titi, mu kaɗai. Ba irin sunan da ba sa kiranmu, mu ne 'yan iska, mu ne matsalar gari, sannan ka riƙa kawo maganar yin gaskiya da kyautatawa? Ya kamata a ce kai me wa'azi ne. Yawon titi bai dace da kai ba.

**ZAKARI:** Na fahimci duk abin da kake nufi. Bai kamata a ce wani ya zartar da wani hukunci a kanmu ba. Ba su san yadda aka yi muka samu kanmu a cikin wannan hali ba.

**SHEHU:** To, ni ban ga laifinsu ba. Ko mu kanmu, ba mu san yadda aka yi muka tsinci kanmu a kan waɗannan titunan birnin masu mummunan hatsari ba.

**ZAKARI:** Shi ya sa ya kamata mu bar wannan barar da muke yi, Shehu. Ba wata rayuwa mai ma'ana a kan abin da muke yi, ba rayuwa ba ce mai kyau. Gwamma mu fara wasan ƙwallon ƙafa. Hakan zai kyautata zukatanmu ya kare su daga jin yunwa.

**SHEHU:** Ka haukace ne Shehu? Kwallo, ƙwallo, ƙwallo dai? Ba wata magana da kake yi in ba ta ƙwallo ba? Wai dole ne kowace magana ta ƙare da maganar ƙwallo? Da safe ƙwallo, da rana ƙwallo, kome dai ƙwallo. Ba zan yi mamaki ba idan kana yawan mafarki. Wannan ƙwallon taka ta tsumma, a cikin mafarki in kana barci a kan katakon da kake kwanciya.

**ZAKARI:** Wai za ka zo mu je ko kuwa?

**SHEHU:** Wato ma ba ka ji duk abin da nake cewa ba ko? To! Ba zan je ba, Zakari! Ni ina buƙatar kuɗi saboda sayen abinci. Ka je ka

yi ta buga wannan sakaryar ƙwallon taka, amma kar ka kuskura ka zo wajena da yamma, ka ce in ba ka burodi da wake.

**ZAKARI:** Ka kuwa san irin yawan kuɗin da ƙwararrun 'yan wasa a duniya ke samu a rana ɗaya kawai? Wai me ma ya sa nake ta damun kaina ina gaya maka wannan? Yanzu sai dai mu haɗu an jima a inda muka saba haɗuwa.

**MAI GABATARWA:**
Sai Zaks, kamar yadda Shehu ya saba kiranshi, ya kama hanyarshi riƙe da sanadiyyar yin arzikinshi a hannunshi, wato ƙwallon tsumma da ya yi daga tsummokarai da ledoji da ya tsinto daga bola. A halin da ake ciki kuma a ɗaya ɓangaren garin Safina, 'yar shekaru goma sha uku, ta iso gidan antinta, tare da dukkan kayanta. Me ya kawo ta? Kuma me za ta taras a babban garin? Bari mu ji yadda za ta kaya.

**Fitowa ta 2: A gidan Anti Lily**
Safina, Anti Lily

**ANTI LILY:** Wane ne? Ina zuwa! … Uhm, me kike buƙata yarinya?

**SAFINA:** Anti Lily? Ni ce fa, Safina! Ai kin san ina tafe ko?

**ANTI LILY:** Laaa Safina! Ikon Allah! Ke ce kika girma haka! Ai ba zan iya gane ki ba idan muka haɗu a kan titi. Shigo, shigo! Sannu da zuwa.

**SAFINA:** Anti, me ya sa kika sa waɗannan manya-manyan kwaɗunan? Mu a ƙauye da guda ɗaya muke amfani.

**ANTI LILY:** Sannu da zuwa birnin Gabas, yarinya! Ai a birni, yawan

kwaɗunan da kike amfani da su wajen kulle ƙofa, shi ne zaman lafiyarki. Kin gane ai, ɓarayi masu fasa ƙofa. To yaya gida, yaya kika baro iyayenki da kuma 'yar'uwata?

**SAFINA:** Duk suna lafiya, sun ce in gaishe ki. La! Kafin in manta, Mama ta rubuto miki wasiƙa. Anti, wallahi duk ƙauyen nan kowa ya ɗauka ke mai kuɗi ce, amma na…na ga...gado ɗaya ne kawai, da teburi, da kuma kujeru biyu, da wannan rediyon.

**ANTI LILY:** Daga zuwanki yanzun nan har kin fara tsarguwata. Lalle ina ganin za mu sami matsala nan gaba. Bari in ga abin da 'yar'uwata ta rubuto mini.

**MAI GABATARWA:**
A yayin da Anti ke buɗe wasiƙar da 'yar'uwarta ta rubuto mata, ba da nisa ba kuma inda masu kuɗi da waɗanda suka yi suna a birnin Gabas suke zaune, John, ɗan shekaru goma sha biyar kuma ɗan sanannen ɗan siyasan nan Honourable Gambo, yana kwance, yana shaƙatawa a kan kujera mai taushi, yana buga wasan ƙwallon ƙafa a na'urarshi ta komfuta.

**Fitowa ta 3: A gidan Honourable Gambo**
Honourable Gambo, John

**JOHN:** Yauwa, ga shi nan, ga shi nan! … *Go! Come on, come on! Shoot* mana! Kash! … Yauwa! *Gooooooal! Winner!*

**HON. GAMBO:** John! John!

**JOHN:** Yauwa Baba, zo ka gani! Zo ka ga abin da na yi. Na doke ƙungiyar da ta fi kowacce a duniya. Yanzu ba wanda ya kai ni! Na fi kowa! *Winner…!*

**HON. GAMBO:** John, wane irin ihu kake yi haka, bayan da komfutarka kawai kake wasa. John! Ana wasan ƙwallo ne a filin wasa ta amfani da ƙafafuwanka, kai, ƙirji da gwiwoyi, ba wai da wasu yatsu biyu ba a allon komfuta. Idan har kana so ka zama ƙwararre, to sai ka yi abin da kake yi yanzu.

**JOHN:** Mene ne? Faɗa min, Baba, me ya kamata in yi? Zan yi duk abin da ya kamata in yi domin ka yi alfahari da ni. Kai tsohon ministan wasannin motsa jiki ne, ya kamata a ce abin a jininmu yake.

**HON. GAMBO:** Hmm, John! Lalle na ga da gaske kake yi. Ina ganin ya kamata in gaya maka wata magana. Ana ta raɗe-raɗi a majalisa cewa akwai wani sanannen ɗan wasa da zai shirya wata gasa a birni. Duk ƙungiyar da ya zaɓa, to za ta je ƙasashen Turai. John, ina son ka kasance cikin wannan ƙungiyar, kuma zan yi duk abin da na ga ya yi don in ga cewa an zaɓe ka. Taso! Taso mu je mu yi wasa! Ya kamata ka fara shiryawa.

**JOHN:** *Wow!* Baba wannan labari ne mai daɗin ji! Kana ganin wane ne ɗan wasan, kuma yaushe ne za a yi? Kana tunanin cewa ya kamata ni ma na shiga?

**MAI GABATARWA**

Sannan, yayin da uba da ɗa suka fice waje don su buga ƙwallo, Zakari kuma ya iso shagon "Shah Electronics" don ya kalli shirin da ya fi so, wato labarin wasanni na rana. Amma ba ƙaramin aiki ba ne saboda duk waɗanda suka zo kallo, sai su riƙa leƙawa ta ƙarfen da ke tagar shagon, don su riƙa kallo a talabijin ɗin da aka ajiye don sayarwa. Zakari ya yi sa'a, don yana ɗaya daga cikin waɗanda suka sami wuri mai kyau na kallo. Bari mu saurari abin da ke faruwa.

**Fitowa ta 4: A shagon "Shah Electronics"**
'Yar jarida (a talabijin), Zakari, Wani mutum

**'YAR JARIDA:** Masu kallonmu, barkanmu da sake saduwa da ku a shirinmu na labarin wasanni. Yau za mu fara ne da gasar ƙwallon ƙafa na ƙalubale na ƙasa. Kungiyar ƙwallon ƙafa ta garin Gabas, zakarun shekarar bara, sun yi canjaras da abokan hamayyarsu ta Wanderers, inda aka tashi wasa ba ci. A wasu wasannin da aka yi a ƙarshen mako…

**ZAKARI:** Kai, ka daina ture ni mana! Na riga ka zuwa nan!

**WANI MUTUM:** Ka koma cikin bolar da ka fito, duk ka cika mutane da wari.

**ZAKARI:** Na ƙi. Wannan wurin kowa da kowa ne, wanda ya riga wani zuwa shi ke nan.

**WANI MUTUM:** Ya kamata irinku duk a kama ku a kulle a gidan yari, kuma a koya muku hankali. Ga dukkan alamu, iyayenka ba su koya maka tarbiyya mai kyau ba.

**ZAKARI:** Kar ka ƙara kawo iyayena cikin wannan maganar, ka ji ko?

**WANI MUTUM:** To shi ke nan, shi ke nan. Ba damuwa! Ma iya ci gaba da sauraren labarin ko?

**'YAR JARIDA:** Daga ƙarshe a cikin labarun namu na yau, ga wani labari mai daɗi ga matasa. Idan kai ɗan shekara goma sha biyu ne zuwa sha shida, kuma kana zaune a birnin Gabas, kuma kana da sha'awar wasan ƙwallon ƙafa, to ga wata dama ta samu da za ka iya nuna bajintarka a cikin mako mai zuwa, ta hanyar shiga wata gasa wadda wani shahararren ɗan wasan ƙwallon ƙafa na duniya ya shirya, kuma ya ƙi yarda a

san ko shi wane ne. Duk ƙungiyar da aka zaɓa, to za ta shiga wani yawon duniya da aka laƙaba wa suna "Manufa ta kawo zaman lafiya" a wani yunƙuri na kawo daidaito da zaman lafiya a ƙasarmu. Za mu ƙara kawo muku wasu bayanan a kan wannan idan muka samu nan gaba…

**ZAKARI:** Kai! Ai kuwa wannan abu ya yi kyau! Wannan wata dama ce da ba zan yarda ta kuɓuce min ba! … Shehu! Shehu!...

**MAI GABATARWA:**

Da wannan ihu na Zakari mai ɗauke da sa rai, tabbaci da kuma ƙwazo, a yayin da ya ruga da gudu cikin birnin Gabas, muka kawo ƙarshen wannan shiri na farko mai taken "Kwallon ƙafa salon Afirka". Yaya Shehu zai ɗauki wannan labari na gasar ƙwallon ƙafan? Yanzu kuma da yake shi ma John na cikin waɗanda suke neman wuri a cikin ƙungiyar da taimakon mahaifinshi, yaya za ta kaya? Kuma kar ku manta cewa, Anti ta buɗe wasiƙar da 'yar'uwarta ta rubuto mata, ko me ke ƙunshe a cikin wannan wasiƙar? Sai a kasance da mu a shiri na gaba domin jin waɗannan amsoshin. Ana iya sake sauraron wannan shirin ta adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.